# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tudun mun tsira – Mai bayani a kan 'yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai
## Kashi na goma sha uku: Shiga ciyawa

Wadda ta rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Magaji: | ɗan shekara 22 |
| Jami'in shige da fice: | ɗan shekara 40 |
| Lami: | 'yar shekara 20 |
| Sa'adatu: | 'yar shekara 35 |
| Charles: | ɗan shekara 45 |
| Ɗan sanda: | ɗan shekara 35 |
| Faisal: | ɗan shekara 19 |
| Roda: | 'yar shekara 25 |

**Mai gabatarwa:**
Masu saurarenmu, barkanmu da sake saduwa a cikin shirinmu na “Ji Ka Karu”. Wannan shi ne kashi na goma sha uku a shirinmu na wasan kwaikwayo a kan ƙaura da matasa daga Afirka ke yi zuwa Turai, mai taken “Tudun mun tsira”. Idan ba mu manta ba, wannan wasa ne a kan rayuwar waɗansu matasa, wato Lami, da Faisal, da kuma Magaji. Mun ji kuma cewa ko da yake akwai damammakin karatu da kuma ci gaban ɗan Adam a Turai, akwai kuma waɗansu abubuwan ƙi, musamman ma dai idan mutum ba bisa ƙa’ida ya shiga Turai ɗin ba.
Sai ku biyo mu cikin shirin namu na yau mai taken “Shiga ciyawa” don jin yadda za ta kasance. Yanzu dai ga mu a ofishin jami’an shige da fice a lokacin da suke ganawa da Magaji.

**Fitowa ta 1: Magaji yana yi wa jami’in shige da fice bayani**

**Jami’in shige da fice:** Wato dai kai ne sabon akarambanar da muka samu ko?

**Magaji:** Akarambana? Ban gane ba, Yallaɓai, me kake nufi da haka?

**Jami’i:** To, ba ga shi ka kurɗaɗo ta cikin jirgin da muke ta fama jigilar kai abinci Afirka ba don ya kawo ka Turai? Ni na kwana biyu ma ban ga abin mamaki irin haka ba, sai kai. Ka ga wannan ya sa ka zama jarimi, ko ba haka ba?

**Magaji:** Ranka ya daɗe, ba haka ba ne. Gaskiya ni ma ban taɓa yin abin da ya ba ni tsoro a rayuwata irin wannan ba.

**Jami’i:** Ko? Saboda me ka ce haka? Ba ga shi ka shigo cikin Turai ba tare da wani ya gan ka ba? Idan aka kwatanta da sauran ’yan gudun hijira da ke zuwa ta cikin ƙananan kwale-kwale, kai ai tafiya taka ta zama ta alfarma. Yanzu akwai kuɗi a hannunka ne?

**Magaji:** Kuɗi kuma? Yallaɓai, kana nufin kuɗi kamar Yuro?

**Jami'i:** A'a, Malam Magaji, ba wai lallai sai Yuro ba, ina nufin zunzurutun kuɗi ko ma na wace ƙasa ne. Kana da su?

**Magaji:** E to, ina da ɗan kuɗi, amma ba masu yawa ba ne. Ka san ni ke kula da gidanmu, kuma gidan yawa ne.

**Jami'i:** Kai ke kula da gidanku? Kana da iyali ke nan?

**Magaji:** Ba ni da aure, amma ina kula da ƙannena maza da mata.

**Jami'i:** Wato dai kana da iyali kuma kana da wadda za ka aura? To, ai kai ba ka yi kama da ɗan gudun hijira ba. Me ya sa kake neman mafaka?

**Magaji:** To, ka san a can ƙasarmu mun yi zaɓe, kuma bayan da aka gama sai tashin hankali ya biyo baya a tsakanin ƙabilun ƙasar. Ni nan na tsere wa tashin hankali ne saboda ana kai wa ƙabilarmu hari.

**Jami'i:** Aha, to, na ji. Yanzu yaya za ka yi da sauran 'yan'uwanka? Ba ka tunanin suna cikin irin wannan haɗarin?

**Magaji:** E to, a'a. Gaskiya dai ina ji musu tsoro, amma na san suna nan ƙalau.

**Jami'i:** Ta yaya za ka yi ka sani?

**Magaji:** Ta yaya? Ai na ga halin da suke ciki.

**Jami'i:** Yaushe ke nan, kana nufin kafin ka zo nan?

**Magaji:** E!

**Jami'i:** To, na ji. Ka ce bayan an gama zaɓe, an samu rikicin addini, ta yaya?

**Magaji:** Gaskiya ba zan iya cewa ba. Na san dai muna da wannan matsala.

**Jami'i:** Wace irin matsala ken an, Malam Magaji? Ban gane ba.

**Magaji:** Matsalar rikicin addini mana.

**Jami'i:** Na ɗauka ma irin rikicin ƙabilanci ne?

**Magaji:** Na ƙabilanci? E, haka ne, na ƙabilanci da na addini ba.

**Jami'i:** To madalla, tambayoyin sun isa haka. Sai dai kuma ina ganin ba ka cancanci a ba ka mafaka ba domin bayanin da ka bayar gaba ɗayansu ba su da kai kuma ba su da gindi. Don haka ban amince da wannan buƙata taka ba. Yanzu maza zan tasa ƙeyarka zuwa gida Afirka, nan ba da daɗewa ba.

**Magaji:** Tsaya, yaya za a yi min haka. Na gaya maka…

**Jami'i:** Shhhh! Shi ke nan magana ta isa haka.

**Mai ba da labari:**

Ba dai abin da Magaji zai iya yi illa ya tashi ya koma ɗakinsa da ke cikin sansanin 'yan gudun hijira saboda ya gaza amsa tambayoyin da aka yi masa, kuma a yanzu yana jira ne a mayar da shi ƙasarsu. To, ko zai yarda da

wannan al'amari?

Can kuma ga Lami, da Sa'adatu, da Charles suna ɗan shaƙatawa a gidan rawa.

**Fitowa ta 2: Lami da Charles da Sa'adatu a gidan rawa**

**Sa'adatu:** Lami, kina jin labarin babanki kuwa? Yaya jikin nasa?

**Lami:** Ina ji mana. An ce aikin da aka yi masa ya yi kyau, kuma likitoci sun ce yana samun sauƙi sosai.

**Sa'adatu:** Madalla, haka ake so! Yauwa, kina ji? Idan kin gama jami'a, muna so ne ki zo ki yi aiki tare da mu a matsayin cikakkiyar ma'aikaciya. Abubuwa za su gyaru. Na san nan da 'yan shekaru Hukumar Shige da Fice za ta ba ki takardar izinin zama na dindindin. Kin ga za ki iya yin duk abin da kika ga dama!

**Lami:** Ai ni har yanzu jina nake kawai. Ganin abin nake kamar a mafarki.

**Ɗan sanda:** Mu 'yan sanda ne, kada kowa ya motsa! … To, ke ce da ma Sa'adatun da ake faɗa?

**Sa'adatu:** E, ni ce!

**Ɗan sanda:** Wannan kuma shi ne tsohon mijin naki ko? Kuma ina ji ku ne kun mallaki wannan gidan rawar ko?

**Charles:** E, haka ne, ranka ya daɗe, mu ne.

**Ɗan sanda:** Wannan yarinyar kuma ita ce Lami Talle? Kuma ɗalibar

jami’a ce wadda ke auren Charles, ko ba haka ba?

**Sa’adatu:** E, haka ne. To ranka ya daɗe, akwai wata matsala ne?

**Ɗan sanda:** Mun daɗe muna bincike a kanku, ku biyun nan. Yanzu za mu tsare ku saboda muna zarginku da shirya auren biza tsakanin ’yan Afirka da kuma Turawa, saboda Turawan su dinga taimaka musu don samun takarda zama ’yan ƙasa. Sannan kuma muna tuhumarku da tilasta su su dinga yi muku aiki a gidan rawarku. Ta haka kuna zaluntarsu kuma kuna danne musu haƙƙinsu. Idan har muka tabbatar da cewa wannan auren da ke tsakanin Lami da Charles na bogi ne, za a raba shi a kotu. Ke kuma Lami Talle, abin da ba mu tabbatar ba shi ne, ko da yardaki aka yi wannan aure, ko kuma tursasa ki aka yi. Ni ban san ta inda kika shigo cikin wannan harka ba. Tun da ba mu da wata shaida a kanki yanzu an sallame ki.

**Lami:** Na gode maka, Yallaɓai, na gode maka sosai!

**Charles:** Ranka ya daɗe, na rantse maka ban san zancen da kake yi a kai ba. Ni ina ganin dai akasi aka samu.

**Sa’adatu:** Kai Charles, ka kwantar da hankalinka! Zargi kawai ake yi. Ka ga ke nan ba mu da wani laifi har sai an tabbatar muna da shi. Ni ban ga wata shaida da ta nuna cewa mun aikata laifi ba. Kana ji? Mu bi wannan jami’i mu yi duk abin da ya ce mu yi.

**Mai ba da labari:**

Lami dai tana cikin tsoro a yayin da ta ga an tasa ƙeyar Sa’adatu da Charles daga cikin gindan rawar a cikin ankwa. To, ko za a same su da laifi? Kuma ko

me Lami take shirin yi? Sai ku ci gaba da saurare.

A ɗaya ɓangaren kuma, a cikin sansanin 'yan gudun hijira, ga Magaji yana zantawa da Faisal wanda bayan da jami'an shige da fice suka gana da shi karo na biyu, ya ga alamun cewa zai samu mafaka. Don haka ga Faisal can yana ba wa Magaji shawara a kan abin da ya kamata ya yi.

**Fitowa ta 3: Magaji ya tsira daga sansanin 'yan gudun hijira**

| | |
|---|---|
| **Faisal:** | Ka tabbata jami'in ya ce maka ba za ka samu mafaka ba? |
| **Magaji:** | Haka ya ce da ni, wai bai yarda da bayanin da na yi masa ba. Ya ce na yi baki biyu, kuma nan da 'yan kwanaki za su mai da ni gida. |
| **Faisal:** | Kana ganin hakan ya fi maka? Ka fi son a mai da kai gida Afirka? In dai kana son ka zauna, yanzu zaɓi ɗaya kawai ya rage maka. |
| **Magaji:** | Zaɓi ɗaya! Wane zaɓi ne wannan? Ai tun da na sha wahala har na zo nan, lallai sai na cimma abin da na faro. Dole sai na sa Lami a idanuna. Yanzu gaya min abin da ya kamata in yi! |
| **Faisal:** | Yanzu tun da ka san cewa ba za ka samu mafaka ba, dole sai dai ka shiga cikin ciyawa. |
| **Magaji:** | In shiga cikin ciyawa? Kana nufin in sulale ke nan ba tare da wani ya gan ni ba? |
| **Faisal:** | Wannan shi nake nufi. Na san akwai haɗari, amma kuma akwai wani wanda na sani, kuma shi ma ya san wani. Idan ka ce masa ni na turo ka, to, zai taimaka maka. Amma |

dole sai ka fara tserewa daga wannan sansanin tukuna. Ka san ni ma na sha tunanin abin da zan yi idan takardata ta neman mafaka ba ta samu shiga ba. Kuma yanzu na san abin da zan yi. Tsaya ma ka ji!

**Magaji:** To.

**Mai ba da labari:**
Ga dai Faisal nan yana yi wa Magaji bayanin inda ya kamata ya je, da kuma abin da ya kamata ya yi. Bayan 'yan awanni, ga Magaji yana tsaye a bakin babban ofishin wannan sansani. Can sai ga wata motar ɗaukar kaya nan ta tsaya a bakin ofishin. Da dai ya fakaici cewa direban motar ba ya kallonsa, sai ya shiga ƙarƙashinta ya maƙale gangam a jikin waɗansu maɗaukai. Yanzu dai ga motar can tana tafiya a kan titunan birnin Turai.

**Magaji:** Mts, ni me ya sa na zo wannan gari ne ma? Sai ka ce ba na cikin hankalina! Ba abin da Allah bai hore min ba a gida? Kai Lami, duk fa wannan wahala da nake sha saboda ke ce! Na san nan ba da daɗewa ba zan kasance tare da ke. Ba zan iya jurewa ba. Bari dai na gani, ko ni, ko su! ... Wayyo bayana, wayyo!

**Roda:** Kai, ƙalau kake? Ayya, ai zub da jini kake yi. Bari mu nemi motar asibiti. Tsaya ma tukuna, wai ina ka nufa ne?

**Magaji:** Bari don Allah, kar ki kirawo motar asibiti ko 'yan sanda! Zan samu sauƙi. Don Allah nan ne babban birni? Gaya min yadda zan kai ga zuwa jami'a.

**Roda:** Babban birni? A'a, ba nan ba ne. Akwai tafiya mai nisa. Tsaya ka ji! Sunana Roda, a nan kusa gidana yake. Zo mu je idan ba ka son zuwa asibiti. Bari zan yi maka magani,

daga nan sai ka yi tafiyarka.

**Magaji:** Na gode, na gode! Wayyo, yi a hankali fa!

**Roda:** Ba nan za ka yi ba, biyo ni!

**Magaji:** Bari na tafi. Lokaci yana ƙure min.

**Roda:** A'a, ba dai a cikin wannan halin da kake ba. Kana zubar da jini fa, kuma kana buƙatar wanka da ruwa mai ɗumi, kuma kana buƙatar abinci. Kai dai biyo ni! Na san duk abin da kake ji. Na yi alƙawarin ba zan cuce ka ba. So nake kawai na taimaka maka.

**Magaji:** Bari don Allah. Ga 'yan sanda nan sun biyo ni! Wayyo!

**Roda:** Kar ka tsorata! Riƙe hannuna mu tafi tare. Yauwa, ya yi haka! … Sannu!...

**Mai gabatarwa:**
To, ko Magaji zai kauce wa haɗuwa da 'yan sanda? Idan ma har ya yi nasarar kauce musu, ai ba shi da kuɗi da kuma takardar izinin shigowa Turai. To, ta yaya ke nan za su haɗu da Lami? To, yaya kuma batun halin da Faisal zai shiga? Idan har aka ba shi mafaka, shin hakan yana nufin duk matsalolinsa sun warware ke nan? Sai ku kasance da mu a kashi na gaba don jin amsoshin waɗannan tambayoyi da ma sauransu.
Muna kuma gayyatarku da ku ziyarci shafinmu na tattaunawa wato facebook.com/dw.lbe don bayyana ra'ayoyinku a kan yanayin rayuwar 'yan gudun hijira waɗanda ba su da takardun izinin shiga Turai, amma sai dai su dinga wasan ɓuya da jami'an shige da fice. Idan kuma kuna son ku sake sauraren wannan shirin da muka gabatar, sai ku ziyarce mu a shafinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Kafin wannan lokacin, sai mu ce sai an jima.